# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Kwallon ƙafa salon Afirka
## Kashi na biyu: Tsakanin wasa mai kyau da mara kyau


| | |
|---|---|
| Wanda ya rubuta: | Chrispin Mwakideu |
| Wanda ya tace: | Ludger Schadomsky da Maja Braun |
| Wanda ya fassara: | Yusuf Idris |


**'Yan Wasa:**

| | |
|---|---|
| Zakari: | ɗan shekara 14 |
| Shehu: | ɗan shekara 14 |
| Anti Lily: | 'yar shekara 33 |
| Safina: | 'yar shekara 13 |
| Mai abinci: | 'yar shekara 20 |
| John: | ɗan shekara 15 |
| Honourable Gambo: | ɗan shekara 55 |
| Metogba: | ɗan shekara 28 |
| Sakataren otel | |

**MAI GABATARWA**:

Masu sauraronmu, barkanmu da sake saduwa da ku a cikin wani shiri na "Ji Ka Karu" wanda muke kawo muku a kan wasan ƙwallon ƙafa. A wasanmu na farko, mun tsaya ne a inda Zakari ya ruga da gudu kan titin birnin Gabas, don ya nemo babban abokinsa Shehu kuma ya ba shi labarin gasar da za a yi, wanda ya ji labari a labarun wasanni da ya kalla. Ita kuma Safina ta baro ƙauye, ta zo wurin antinta wadda ke zaune a birnin Gabas, haɗe da wata wasiƙa daga mahaifiyarta. Sannan shi kuwa John, ya sami labarin gasar ƙwallon ƙafa da za a yi ne kai tsaye daga mahaifinshi. Sai ku kasance da mu don jin yadda za ta kaya a yau, a cikin shirinmu mai taken "Tsakanin wasa mai kyau da wasa mara kyau". Za mu faro shirin na yau ne daga inda Anti Lily ke karanta wasiƙar da 'yar'uwarta ta aiko mata.

**Fitowa ta 1: A gidan Anti Lily**

Anti Lily, Safina

**ANTI LILY:** To, bari mu ji abin da 'yar'uwata ke cewa.
*Zuwa ga Lily. Ina fata wannan wasiƙar za ta same ki cikin ƙoshin lafiya. Mun daɗe ƙwarai da gaske da muka.. blah blah blah … saboda haka tun da ba mu da halin sa Safina a makaranta, kuma mu kula da ita yadda ya kamata a nan ƙauye, ga ta nan mun turo miki ita. Yarinya ce mai ƙwazo, kamar yadda za ki gani, sannan tana da sha'awar buga wasan ƙwallon ƙafa sosai. Don Allah ki kula da ita sosai. Ki huta kafiya. Daga 'yar'uwarki Maman Safina.*
Kai!

**SAFINA:** Anti, me yake ba ki dariya ne? Ba ki ma karanta wasiƙar ba har zuwa ƙarshe!

**ANTI LILY:** Wannan dai zolaya ce da aka ce kina da sha'awar buga ƙwallon ƙafa. Da wasa ne sam kuma da gangan, ko kuwa?

| | |
|---|---|
| **SAFINA:** | A'a, gaskiya ne! Kuma ba wai ina buga ƙwallon ba ne kawai, na ƙware sosai a kan haka, Anti, bari in nuna miki. Akwai filin wasan ƙwallon ƙafa a nan kusa? Na ma fi wasu matasan iya murza ƙwallon a ƙauyen. Wata rana ma har na… |
| **ANTI LILY:** | Ke! Ke Safina! Saurare ni da kyau! Zan faɗa miki wannan ne sau ɗaya kawai, ba sau biyu ba, sau ɗaya tak! Ba wata magana ta wasan ƙwallo har iya tsawon zamanki a gidana, kuma a ƙarƙashin kulawata! Kin ji ni sosai? Ke fa mace ce! Sannan idan ba ki fahimci haka ba har yanzu, to nan da 'yan shekaru kaɗan za ki zama babbar mace. Kwallon ƙafa wasa ne na maza sakarkaru, waɗanda ba wani abin arziki da za su iya ƙullawa. Bayan haka ma, me kike ganin maƙwabtana za su iya tunani, idan suka gan ki kina ta gudu tare da maza da sunan buga ƙwallo? Ai sai in zama abin dariya a birnin Gabas. Sam ba zan yarda da wannan ba. |
| **SAFINA:** | To amma, amma… |
| **ANTI LILY:** | Ke! Kar ki cika ni da wata "amma, amma"! Maza ki ɗauki jakarki ki kai ta can gefen. Sannan ki zo ki taimake ni in ƙarasa abincin rana. Kwallo? Ke kin ji! Duk a rasa wasan da za a yi? Wai me yake faruwa ne a wannan duniya tamu? |

**MAI GABATARWA:**
Wannan ba irin tarbar da Safina ta tsammaci za ta samu ba ke nan. Amma da yake tana da ladabi da biyayya, cikin hanzari sai ta kwantar da hankalinta, ta fara taimaka wa antinta. Yanzu kuma bari mu ji yadda abokin Zakari, wato Shehu, zai karɓi labarin da Zakari ya zo mai da shi.

**Fitowa ta 2: A garin Gabas da yamma**

Zakari, Shehu, Mai abinci

**MAI ABINCI:** Burodi da wake! A sayi burodi da wake!

**SHEHU:** Kawo guda ɗaya nan!

**MAI ABINCI:** To Malam, ina zuwa.

**SHEHU:** Ga ni nan! Yauwa, sannu!

**ZAKARI:** Shehu! Shehu! Shehu! Na san ba za ka yarda da abin da...

**SHEHU:** A'a, a'a, a'a! Malamin ƙwallon ƙafa na titin birnin Gabas. Wannan abincin da ka gani, to gumina ne, kuma ba za ka sami ko da loma ɗaya ba. Tun da dai kai rayuwarka ta ta'allaƙa ne a kan abu ɗaya: ƙwallon ƙafa. Barcinka ƙwallo ne, mafarkinka ƙwallo ne, maganarka ƙwallo ne a kowane lokaci. To shi ke nan, sai ka je ka ci ƙwallon!

**ZAKARI:** Ka ga, ni ba abincinka ne ya kawo ni nan ba, amma kuma gaskiya da na ga kwanon waken can, sai na ji ina jin yunwa. Amma dai ka saurare ni, duk da na san ba za ka yarda da abin da na ji ba kuma na gani a shagon "Shah". Kai! A labarun wasanni yau akwai abubuwa da yawa, domin sun ce…

**SHEHU:** To tsaya, tsaya! Gwamma abin da za ka faɗa ya kasance mai kyau. Mai ba da abinci, don Allah ƙaro mana wani cokalin. To, ci gaba!

**MAI GABATARWA:**

A yayin da Zakari yake gaya wa Shehu labarin da ya ji a cikin labarun

wasannin a game da wannan gasar, a wani bene kuwa a kusa da su, wata mota ce mai kyan gaske, take shiga inda ake ajiye motoci a ɗaya daga cikin otel-otel mafi kyau a birnin Gabas. Zaune a cikin motar, Honourable Gambo ne da ɗanshi John. Ko wa suka zo gani? Bari mu saurara mu ji.

**Fitowa ta 3: A otel**

Honourable Gambo, John, Metogba, Sakataren otel

**HON. GAMBO:** John, kamar yadda muka tsara a mota, ka ƙyale ni in yi magana. In ba ya tambaye ka wani abu ba, kar ka ce kome. Ka ji ko?

**JOHN:** E, na ji Baba. Ka san ɗakin da yake ne?

**HON. GAMBO:** John, na sani mana. Kana manta cewa ni ɗan majalisa ne. Jama'a fa Honourable Gambo suke kirana. Ni tsohon ministan wasanni ne kafin tashin hankalin da aka yi. Kira ɗaya zan yi ya biya min buƙata. Na san lambar ɗakinshi, kuma na san tsawon lokacin da zai kasance a nan. Abin da kawai ban sani ba shi ne, wane ɗan wasa ne, amma wannan ma nan ba da daɗewa ba za mu sani. Bayan haka ma, na san duk mutanen da zai yi aiki da su. Ba za ma mu daɗe a kan abin da ya kawo mu ba.

**JOHN:** Amma Baba, kana ganin cewa zai yi…ina nufin, ka san cewa…to kuma idan ya…

**HON. GAMBO:** Kai! Kai John, ka kwantar da hankalinka! Kasar nan fa a hannunmu take. Kome da kowa, har da ƙwallon ƙafa.

**SAKATAREN OTEL:** Sannu da zuwa Honourable. Ga wuri nan ka zauna. Yanzu zan kira baƙonmu in sanar da shi cewa ka iso. Ko

kana buƙatar wani abin sha ne?

**HON. GAMBO:** A'a, na gode. Ina da wani wurin da za ni yanzun nan saboda haka ba zan daɗe ba. Amma ko za ki ba ɗana lemo ya sha.

**SAKATAREN OTEL:** Yanzun nan, yallaɓai. Bari in fara kiran baƙon namu tukuna.

**METOGBA:** Alo? Waye?

**SAKATAREN OTEL:** Yallaɓai, barka da warhaka, daga *reception* ne. Ka yi haƙuri na dame ka, amma kana da baƙo ne da yake son ganinka.

**METOGBA:** Baƙo? Wane irin baƙo? Ni ba ni da wani baƙo da nake *expecting* a yanzu. Sai gobe za a yi taron 'yan jaridun, kuma na ba da oda cewa ba na son kowa ya dame ni kafin wannan lokacin.

**SAKATAREN OTEL:** Na gane, yallaɓai. Amma baƙon na musamman ne.

**METOGBA:** Hmm. To wane ne? … To shi ke nan, ki ce mai zan sauko nan da minti goma sha biyar.

**SAKATAREN OTEL:** Uuuhm, yana ɗan hanzari ne, yallaɓai, wataƙila ko…

**METOGBA:** Kin ga Malama, minti goma sha biyar na ce. Ko ya jira, ko ya tafi.

**MAI GABATARWA:**

Na san cewa mai sauraro na tunanin wane ne wannan ƙwararren ɗan wasan, wanda har yake da ƙarfin zuciyar da zai ajiye mutum kamar Honourable Gambo yana jiransa. To dai ba kai kaɗai kake irin wannan tunani ba. Ni ma

nan ina irin wannan tunanin naka. Amma ka daina damun kanka, saboda nan ba da daɗewa ba za mu gano ko wanene. A yayin da mintoci ke ta shigewa a inda Honourable Gambo ke jira, a gidan Anti kuwa, Safina na gab da fuskantar wani abin mamaki daga antinta.

**Fitowa ta 4: A gidan Anti Lily da daddare**

Anti Lily, Safina

**ANTI LILY:** Safina! Safina!

**SAFINA:** Na'am, Anti.

**ANTI LILY:** Taimaka min da wannan rigar, na kasa jan *zip* ɗin sama. Yi sauri, na kusa makara zuwa wurin aiki. … Wash! Wai, ya kamata in fara rage ƙiba. Yaya kika gan ni? Na yi kyau?

**SAFINA:** E Anti, kin yi kyau ƙwarai da gaske, amma rigar... Anya ba ta ɗan dage ba kuwa? Sannan kuma, Anti, ina za ki je da wannan daren? Wane irin aiki kike yi?

**ANTI LILY:** Ke, yi min shiru! Da farko dai ban tambayi ra'ayinki a kan rigata ba. Na biyu kuma, ba na son yawan tambaye-tambaye, kin gane? Kar ki manta ki kulle dukan makullan, kin ji ko?

**SAFINA:** Gaskiya tsoro ya kama ni. A tsorace nake. Anti Lily, ni ban taɓa kasancewa ni kaɗai ba ƙwallin ƙwal a duk rayuwata.

**ANTI LILY:** Kar ki ji tsoro, 'yar yarinya, ke dai ki yi abin da na gaya miki. Kar ki buɗe wa kowa ƙofa, sai kin ji muryata. Sai an jima. Na bar abinci ki ɗumama in kin ji yunwa, kin ji ko?

**SAFINA:** Sai kin dawo, Anti.

**ANTI LILY:** To, sai na dawo.

**MAI GABATARWA:**
A yayin da Safina ta kulle dukkan ƙofofin gidan, sai ta shiga tunanin inda antinta za ta je. Sannan a yayin da kuma take ta shiga ruɗani a cikin birni, kuma tana juyayin rashin yin wasanta na ƙwallon ƙafa, sai muka kawo ƙarshen kashi na biyu na wannan shiri namu a kan wasan ƙwallon ƙafa. Sai a kasance da mu a shiri na gaba domin jin ko wane ne ƙwararren ɗan wasan nan da ya ƙi yarda a san shi, da kuma yadda zai ɗauki buƙatar da Honourable Gambo ya zo mai da ita. Kuma kar ku manta, Zakari ma yana nan yana shiri ya shiga wannan gasar. Idan kuna son sake sauraron wannan shiri ko kuma aiko da tsokaci, kuna iya ziyartarmu a adireshinmu na yanar gizo, wato www.dw-world.de/lbe.